۲۰۸۲۱۹۲

بسم الله الرحمن الرحیم

www.ketab.ir

سرشناسه: ضرابی‌زاده، بهناز، ۱۳۴۷ - Zarrabi Zadeh, Behnaz
عنوان قراردادی: دختر شینا: خاطرات قدم‌خیر محمدی‌کنعان همسر سردار شهید حاج ستار ابراهیمی‌هژیر. هوسایی
عنوان و نام پدیدآور: Diyar Shina by Bahnar Dharrabi Zade translated by Jamilu Yusif Katsina
مشخصات نشر: قم: نورالامین، ۱۳۹۸= ۲۰۱۹ م.
مشخصات ظاهری: ۲۸۲ص.؛ ۱۴/۵×۲۱/۵ س‌م.
شابک: ۸-۹۹۸۶۷۹-۶۰۰-۹۷۸
وضعیت فهرست نویسی: فیپا
یادداشت: هوسایی.
موضوع: کنعانی، قدم‌خیر، ۱۳۴۱ - ۱۳۸۸.
موضوع: Kanaani, Ghadam Kheir
موضوع: ابراهیمی هژیر، ستار، ۱۳۳۵ - ۱۳۶۵.
موضوع: Ebrahimi Hazhir, Sattar
موضوع: همسران شهیدان -- ایران -- خاطرات
موضوع: Martyrs' spouses -- Iran -- Dairies*
موضوع: جنگ ایران و عراق، ۱۳۵۹-۱۳۶۷ -- شهیدان -- سرگذشتنامه
موضوع: Iran-Iraq War, 1980-1988 -- Martyrs -- Biography
موضوع: جنگ ایران و عراق، ۱۳۵۹-۱۳۶۷ -- شهیدان -- داستان
موضوع: Iran-Iraq War, 1980-1988 -- Martyrs -- Fiction
شناسه افزوده: یوسف کاتسینا، جمیل، مترجم
شناسه افزوده: Yusif Katsina, Jamilu
رده بندی کنگره: DSR۱۶۲۹
رده بندی دیویی: ۹۵۵/۰۸۴۳۰۹۲
شماره کتابشناسی ملی: ۶۰۳۵۵۱۴
NBP۲۰

■ همه حقوق برای ناشر محفوظ است ■
■ هرگونه نسخه‌برداری اعم از کپی‌برداری و بازنویسی و انتشار، اسکن، ذخیره کامپیوتری، ترجمه به زبان‌های دیگر ■
■ و ساخت فایل صوتی کتاب، بدون مجوز کتبی از ناشر ممنوع، شرعاً حرام و از طریق مراجع قانونی، قابل پیگیری است. ■

**دختر شینا**

مؤلف: بهناز ضرابی‌زاده
مترجم: جمیل یوسف
چاپ اول: ۱۳۹۸ش / ۱۴۴۱ق/۲۰۲۰م
ناشر: نورالامین
چاپ: نارنجستان   قیمت: ۴۲۰۰۰۰ ریال   شمارگان: ۵۰۰

● مدیر انتشارات: مصطفی نوبخت
● ناظر گرافیک: مسعود مهدوی
● مدیر تولید: جعفر قاسمی ابهری
● ناظر چاپ: نعمت‌الله یزدانی
● ناظر فنی: علی عبادی‌فرد
● صفحه‌آرایی: علی عبادی‌فرد

www.ketab.ir

# Diyar Shina

Behnaz Zarabi Zadeh

**Fassarar**

Jamilu Yusif

www.ketab.ir

Mutanen wannan zamanin suna cikin tsananin hakikanin kishirwar bukatuwa zuwa ga sanin musulunci na asali a wannan iskar mai kadawa, a daidai lokacin da da yawa suna ganin cewa ai yanzu muna a wani zamani ne na karshen duniya, karkata zuwa ga addini da ainahin sakon addinin wani abu ne da yake ta habbaka cikin gaggawar da take da ban-mamaki, to a wannan tsukin, musulunci yana da kaso mai tarin yawa na wannan karkatar da ake yi zuwa ga addini, shin mai zai hana faruwar hakan? Alhali musulunci addini ne na rayuwa, mai yada adalci da nuna kauna ga 'yan adamtaka ba tare da nuna bambancin jinsi ba, mutumin wannan zamanin wanda ya gano abin nan mai tarin kimar da ya bace masa, a bangare guda kuma yawaitar kayan kallo da kafafen sadarwar na zamani masu ba da labarai da yada sakonni ba dare ba rana sun zama musabbabi na yawaitar sababbin tambayoyi da shubuhohi, wadanda a can baya kadan ko tunaninsu bai zo wa ga mutane. Wannan fantsamar ta bayanai da sakonni, ba ma dai kamar kafafen sada zumunta na zamani a mafi yawancin lokuta suna katange mutum daga yin lafiyayyen tunani kuma suna zama dalili na sanin da yawan abubuwa bisa kuskure ko kuma fahimtarsu a gurgunce, musamman ma dai sanin ilimummuka na addini.

A saboda haka, tabligi da isar da sakonni masu tasiri na musulunci na asali, sakonnin da suke dauke da muhimman lamurra, nauyin yada su yana wuyayen gabaki dayan malamai da daliban ilimi. Kuma ma damar ba a yi aiki tukuru tare da basira domin Allah ba, saboda a samu a isa ga wannan hadafin, to lallai wannan babbar yunkurowa, farkawa tare da karkatowar da al'umma ta yi zuwa ga addini a wannan zamanin, zai kuwa tafi a iska.

Cibiyar <Nurul Amin> a nata bangaren tana bakin kokarinta wajen ganin ta yada sakon addinin musulunci na asali a bisa tsari mafi dacewa, kuma a daidai wannan gaba, domin ganin an kara inganta ayyukan wannan cibiya, cibiyar a shirye take ta karbi dukkan shawarwari da neman gyara na kurakuran da masana suka gani daga garemu.

www.ketab.ir

# ABIN DA LITTAFIN YA KUNSA

GABATARWA ........................................................................7
FASALI NA FARKO ..............................................................13
FASALI NA BIYU....................................................................19
FASALI NA UKU......................................................................23
FASALI NA HUDU ..................................................................35
FASALI NA BIYAR..................................................................45
FASALI NA SHIDA .................................................................51
FASALI NA BAKWAI...............................................................57
FASALI NA TAKWAS .............................................................63
FASALI NA TARA ..................................................................81
FASALI NA GOMA..................................................................95
FASALI NA SHA DAYA .......................................................105
FASALI NA SHA BIYU..........................................................123
FASALI NA SHA UKU...........................................................129
FASALI NA SHA HUDU .......................................................137
FASALI NA SHA BIYAR.......................................................163
FASALI NA SHA SHIDA .......................................................193
FASALI NA SHA BAKWAI....................................................227
FASALI NA SHA TAKWAS ..................................................245
FASALI NA SHA TARA ........................................................255
SHAFIN HOTUNA ................................................................267

www.ketab.ir

# GABATARWA

A raina na ce ni mai zai hana na rubuta tarihin rayuwar wannan matar. Tun tuni na riga na kuduri aniyar yin hakan, da na buga waya (gidanki), sai ke da kanki ki ka amsa wayar. Na yi tsammanin zan yi waya ne da wata mace dattijuwa wadda shekarunta suka dan mika. Amma sai lamarin ya daure min kai, saboda lallai muryarki ta matashiyar mace ce tsaf. To da farko sai na yi tsammanin ko muryar 'yarta ce, don haka sai na ce: "Ina son in yi magana da matar alhaji Sattar ne". Sai ki ka yi dariya ki ka ce: "Ai ni ce da kaina"!

Na fara samun labari dan kadan ne a kan halin da ki ka samu kanki a ciki, daga ciki akwai cewa ke kadai dinki, ki ka yi rainon 'yan kankanan yara har guda biyar, bayan shahadar mijinki alhaji Sattar, amma kin dandani dacin wahala kin kuma ji jiki gaskiya!

A raina na ce da gaske ita din ce kuwa da kanta, ni kam sai na rubuta tarihin rayuwar wannan matar, kuma na shirya tsaf. Amma sai ki ka ce: "Ni ba ahalin tambayoyi da tattaunawa ba ce". To amma dai duk da hakan ki ka bayar da lokacin da za a yi zama na farko. Wanda lokacin nan ya kasance daya ne ga watan 2 na shekara ta 1388 Shamsiyya.

A lokacin ana cikin kakar tumaturi. Ina zo wa gidanki; ina zama ni da ke muna fuskantar juna. Ina kunna na'urar daukar

sauti (mp 3), kina ba ni labari dangane da kanki, mahaifinki, mahaifiyarki, kauyenku mai cike da dausayi da kuma yarintarki. Har ki ka isa ga labarin alhaji Sattar da yakin da suka yi – wadda wannan din gaba daya sun cakude da juna ne - wadda wannan yaki ya kallafa miki wahalhalu masu nauyi a cikin dan karamin gidanki da raunanan kafadunki, wato ina nufin ke Kadame-khair Muhammadi Kan'an. Sai dai fa duk ba a da labarin wannan abin da ya faru gare ki.

Ke kina fada, ni kuma ina sauraro, kikan yi dariya a wasu lokutan ni ma nakan yi, kikan yi kuka ni ma haka. A cikin watan Ramadan muka kammala tattaunawar. Kin yi farin ciki, domin za ki samu damar yin azuminki hankali kwance. A karshe sai ki ka ce: "Ba komai nake son in fada ba, amma ga alamu kusan komai da komai din ma na riga na fada". Amma fa ni na fi ki yin farin ciki. Sai na tafi ga batun rubuta tattaunawar.

Mun yanke cewa idan na kammala rubuta labarin, in kawo maki shi kammalallensa gabadaya ki karanta, saboda idan an tsallake wani abu, in gyara; sai dai lokacin da hakan ya faru, gabadayan lamari ya riga ya rikirkice.

Ina samun labari, a gigice na kamo hanya na zo wajenki dubiya; amma fa ban zo dauke da takardu ba, a'a na zo ne dauke da kayan marmari na gwangwani da ruwan 'ya'yan itace (juice), wannan ya kasance ne a ranar 10 ga watan Dey, 1388 shamsiyya (wato daidai da 31 ga December 2009 miladiyya). Na zo na same ki kina kwance a kan gado, idanuwanki a bude, kina ta kallona amma ga alamu ba ki shaida ni ba. Sai na cika da mamaki, sai na ce: "Sake dai duba wa Kadame-khair, ni ce fa; Darrabi-zade, za ki iya tunawa a lokacin kakar tumaturi. Ke ki na ba ni labari, ni kuma nakan yi ta cin koren tumatiri, saboda dan tsami-tsamin da tumaturin yake da shi sai nake amfani da wannan damar ina runtse

idanuwana don kar ki lura da hawaye sun cika su. Sai dai ki sani ba na zo ne don in tayar maki da damuwarki da bakin cikinki ba".

Kikan ce: "Farin cikina shi ne cewa bayan tsawon shekarun nan, sai ga shi an samu wata mata ta zo ta zauna muna fuskantar juna, domin ta ji labarin kuncin rayuwa da ni kadai na samu kaina a ciki na tsawon shekaru, bakin ciki da damuwar da ban taba fada wa wani shi ba". Kikan ce: "Idan ina ba ki labarin alhaji, sai tunaninshi ya dinga fado min a zuciya cike da damuwa da kuncin rashinsa. Shekara takwas na yi ina rayuwa a tare da shi, amma ko sau daya zuciyata ba ta taba samun damar yi mashi gamsasshen kallo ba. Ba a taba samun lokacin da muka yi zama a wadace irin na miji da mata ba, ga shi mun kasance masu kaunar junanmu, amma ko da yaushe muna nesa da juna. Ina mai tabbatar maki da cewa a cikin wannan shekarun takwas, ba a samu wasu watanni a jejjere da muka kasance kusa da juna ba. Alhaji ya dai kasance mijina ne amma ba mallakina ba ne. Ko da yaushe 'ya'yana wata 'yar dama suke jira, hatta tun a lokutan da yake raye ma, to haka kuma a bayan shahadarshi, sai ki ji suna cewa mama, babannin dukkan dalibai suna zuwa makaranta wajensu, to mu wai mai ya sa ba mu da baba ne?! Nakan ce masu, amma dai ai kuna da mama ko. Yara biyar nake tasawa gaba, sai mu tafi mu raka Hadiza zuwa makaranta. Makarantarsu Ma'asuma da yamma ake zuwa. Azahar na yi sai mu biyar dinmu mu dunguma mu tafi dauko Hadiza lokacin sun tashi daga makaranta. Sai mu shida mu sake dunguma mu tafi rakiyar Ma'asuma makarantarsu, yamma na yi sai mu sake dunguma mu duka mu tafi dauko ta, a haka a haka dai labarin yake ta maimaituwa, gobe da jibi da gata….."

Nakan zubar da hawaye idan kina ba ni labarin lokacin sanyi dusar kankara tana sauka da kuma yasar dusar kankarar da ki ke yi daga kan rufin dakuna haka ma ta tsakar gida.

Ya ke kawata abin kaunata, kin yi rainon 'ya'yanki har zuwa girmansu, danki ne kawai da ki ka aurar yake zaune tare da ke, amma 'ya'yanki 'yan mata kin aurar da su, suna gidajen mazajensu cikin annashuwa, yanzu damuwarki kawai wannan ta karshen.

Ki tashi. Har yanzu labarinki bai gama kammaluwa ba, na fa kunna mp 3, me ya sa ba za ki yi magana ba ne?! Mai ya sa ki ke min irin wannan kallon haka?!

'Ya'yanki 'yan mata sai kuka suke yi ta yi a gabanki, suna cewa: "Sai yanzu muka fahimci ashe mama a 'yan shekarun nan ba ta da lafiya, amma saboda mu, ba ta ce komai ba. Tana gudun kar - mu sani - mu shiga damuwa. Tana cewa ku matasa ne yanzu ku ka fara sabuwar rayuwa, kuma rayuwarku tana garawa kamar ta saura. Bana son saboda rashin lafiyata, in rusa maku naku jin dadin. 'Yar uwarki tana cewa: "Wannan tsinanniyar rashin lafiyar…".

Sai na ce a'a, a'a ba na son wani ya yi magana in ba Kadame-khair ba. Kadam abin kaunata! Ni fa ban lamunce ba. Dole ki kammala bayar da labarin rayuwarki. Domin kin fadi komai dangane da rayuwar alhaji. To yanzu abin da ya rage shi ne tarihinki, juriyarki, hakurinki da sadaukarwarki, amma kuma ga shi kin kamu da tsananin rashin lafiya kuma kin yi shiru. Mai ya faru ne ba ki shaidani ba?! Ki tashi, dole ne a karasa sauran labarin nan fa. Ki tashi, na riga na kunna mp 3 fa. Kuma ga ni zaune ina fuskantarki, ki daina yin zuru kina kura min idanu kawai!

Behnaz Darrabi-zade

Lokacin Bazarar (Summer) Shekara ta 1390 shamsiyya (2011 miladiyya).

www.ketab.ir

Suna: Kadame-khair Muhammadi Kan'an

Haihuwa: 17/2/1341 shamsiyya (May 1962 miladiyya), a kauyen Kayesh, Rizen, jahar Hamadan

Aure: 13/8/1356 shamsiyya (4 Nob. 1977 m)

Mutuwa: 17/10/1388 shamsiyya (7 Jan. 2010 m)

Suna: Alhaji Sattar Ibrahimi Hajir (Kwamandan Bataliya ta 155 Sojojin Ansarul Husain {as})

Haihuwa: 11/8/1335 shamsiyya (1956 m), a kauyen Kayesh, Rizen jahar Hamadan

Shahada: 12/12/1365 shamsiyya (3 March 1987 m), a Shalamce, (Amaliyyar Karbala 5)

www.Ketab.ir